# NAZARIN BAYANAI A KAN MASU SHA'AWAR SHIGA GWAJIN DA KUMA WAKILANSU

| | |
|---|---|
| **Taken Nazari** | Matsayin Asprin da losartan da simbastatin a jiki majinyacin Kwarona bairos da ke a asibiti: gwajin sakamako na canki-canka a mabambantan qasashe (CRASH 19) |
| **Lambar takarda/kwanan wata** | 1.0, 23/04/2020 |

## Gayyatar shiga:

Wannan asibiti yana shirin gudanar da wani nazari domin samar da maganin cutar KWABID-19. Muna gayyatar matasa yan shekara 40 ko fiye wanda aka kwantar a asibiti a sakamakon zargi ko tabbatar da kamuwa da cutar Kwarona don shiga wannan bincike na nazari. Wannan takarda tana dauke da cikakken bayani game da wannan bincike da manufarsa da hadari ko ribar shiga wannan bincike. Idan ka/kin yarda z aka/ki shiga wannan bincike za mu buqaci ka/ki sanya hannu a kan takardar amincewa.

## ABUBUWAN DA SUKA KAMATA KA/KI SANI GAME DA WANNAN BINCIKE:

### 1) Don me za a gudanar da wannan binciken?

Likitocinka suna zargi ko kuma sun tabbatar cewa kana dauke da wata cuta mai suna Kwabid-19. Wannan ya faru ne sakamakon hadu da kwayar cutar SARS-CoV-2 ko kuma korona bairos a taqaice. Kasani cewa 8 daga cikin 10 na masu dauke da kwarona bairos suna samun sauqi a gida ba tare da sun je asibiti ba. Wadanda kuma aka kwantar a asibiti sukan samu sauqi, amma wasunsu kuma suna buqaqatar kula ta musamman da ya hada da iskar oksijin ko injin jan-limfashi kafin su warke duk da cewa wani kaso daga cikinsu ba su ma samun sauki.

A yanzu haka babu wani takamaiman magani don yaqar kwarona duk da yake ana ta qoqarin samar da wadansu. Ana gudanar da wannan bincike domin gano cewa idan aka tallafe shi da qarin magungunan da kan iya warkar da cutar da kan shafi zuciya da huhu ko za a iya kyautata yanayin majinyaci ko kuma ya warke.

### 2) Mece manufar wannan bincike?

Manufar wannan nazari ita ce kwatanta nau'o'in magunguna uku mabambanta kuma sanannu a vangaren warkar da cutar zuciya ko matsalar numfashi a gani ko za su iya yin amfani wajen warkar da majinyaci da ke dauke da kwarona. Tin da wadannan magunguna na gwaji ne babu wanda ya san ko za su yi tasiri wajen taimakon waraka ga majinyaci mai dauke da kwarona fiye da kulawa da kake samu a asibiti(wadda kowa ma yake samu).

Nau'o'in magungunan da za baka/ki qari a kan ainihin kulawar da kake samu a asibiti sun hada da:

- Aspirin (wanda aka fi amfani da shi waje hana bugun zuciya ko shanyewar jiki).
- Losartan (wanda aka fi amfani da shi domin maganin hawan jinni da kare qoda da rage damuwar zuciya).
- Simvastatin (an fi amfani da shi don rage kitse).
- Hada aspirin da/ko losartan da/ko simvastatin

The NHREC assigned number is: NHREC/01/01/2007
Approval dates: 21/05/2020to 20/05/2021.

- Kulawar yau-da-kullum ba tare da wani sabon magani.

### 3) Wa zai gudanar da nazarin?

Mai gudanar da wannan bincike su ne taron masu bincike a “London School of Hygien and Tropical Medicine” (Jami’ar Birnin London) a qasar Turai. Likitoci da Ma’aikatan jinya a fadin duniya za su shiga a yi da su.

### 4) Wa binciken ya shafa?

Marar lafiya da ya kai kimanin shekara 40 da haihuwa kuma likita yana zargi ko ya tabbatar masa cewa ya kamu da cutar kwarona. Ba za a sanya majinyacin da likitansa ya tabbatar magungunan da za yi amfani da su a wannan gwaji ba su dace da shi ba saboda wadansu dalilai kamar idan yana da matsala da daya daga cikin magungunan. Haka majinyacin da yake kan injin jan-numfashi ba zai shiga cikin binciken ba. Kimanin majinyata 10,000 a fadin duniya za su shiga cikin wannan bincike, don haka shawara ta rage gare ka ko ka shiga, ko ka bari.

### 5) Me zai faru nan gaba idan na amince na shiga wannan bincike?

Idan har ka amince ka shiga wannan bincike za a nemi ka cike takardar amincewa. Sannan za a shigar da taqaitaccen bayanin game da lafiyarka da kuma yanayin maganinka cikin kwamfiyuta. Kwamfiyuta zai ta fitar da bayani nan take game rukunin maganin da ya dace da kai. A kowane yanayi, wannan zai hada da kulawar yau-da-kullum a asibiti. Kuma za a samu qarin magunguna da za baka ta baki idan kuma jikin ya yi nauyi sai a baka ta cikin mesar dura wa marar lafiya abinci. Ko kai ko likitanka ba mai ikon fadar irin maganin da za baka. Idan aka dara ka akan magani daya ko biyu ko uku za ka yi ta sha ne har na tsawon kwanaki 28 ko kuma idan an sallame ka daga asibiti, cikin biyu wanda ya fara zuwa. Za shigar da qarin bayani game da lafiyarka cikin kwamfiyuta amma ba buqatar a ziyarce ka bayan sallama daga asibiti.

### 6) Mene ne amfanin kasancewa cikin wannan bincike?

Ba mu sani ba ko wadannan magunguna suna da wani qarin amfani a jiki. Wannan magani na gwaji ta yiwu ba zai taimakeka ba kai-tsaye, amma zai yi amfani ga wani majinyaci nagaba.

### 7) Wane irin hadari wannan bincike yake da shi?

Bayan ‘yan matsaloli da aka sani na wadannan magunguna da suka hada da: cushewar ciki da zubar jini da hajijiya babu wata matsala mai tsanani. Sannan ka/ki tuntuvi likitan asibitinka in ana buqatar qarin bayani. Da zarar ka shiga wannan gwaji kai/ke da likitanka/ki za ku san wane irin magani kwamfiyuta ta tanadar maka. Likitanka ya riga ya saba amfani da wadannan magunguna wajen warkar da marasa lafiya don haka ya sani sosai ko da akwai wata illa da za lura da ita yayin gwajin.

### 8) Zan iya dakatar da gwani ko fita daga binciken sanda nake so?

Eh, idan har likitanka yana so a dakatar da wannan gwaji kana da damar fita. Idan kuma ba ka son a dauki qarin wani bayani game da kai kana da damar fada(sai dai masu bincike na iya sarrafa sauran bayanan da aka dauka kafin wannan lokaci).

### 9) Idan ina da tanbaya ko kuma matsala wa zan tuntuva?

Idan kana da tambaya ko matsala sai ka tuntuvi ma'aikatan lafiya na asibitinka. Akwai qarin bayani game da wannan bincike a wannan adreshi kamar haka: (http://crash19.lshtm.ac.uk/)

### 10) Wane bayani kukan voye na sirri?

Duk wani bayani game da lafiyarka za a voye shi. Mutanen da kan iya samun bayaninka su ne likitocin da ke yin bincike da ma'aikatan cibiyar bincike na "London School of Hygiene and Tropical Medicine (Jami'ar Birnin London)" da hukumomin da kan sa ido domin tabbatar da an yi aikin daidai. Wadansu asibitocin ba za su iya ajiye takardar amincewa a wajensu ba don gudun yaduwar cutar kwarona biaros. A irin wannan yanayi za a aji taqardar amincewa mai dauke da sunanka da sa hannunka da a cikin kwanfiyuta a cibiyar binke a London. Za a yi taka-tsantsan wajen adana wannan bayani kuma ba za turawa kowa ba.ba za a yi amfani da sunanka ba wajen fitar da sakamako.sanarwa ta sirri na nan a yanar-gizo.

### 11) zan iya shiga wannan aiki?

Zavi ya rage naka/ki, shiga ko bari, domin ganin dama ce. Ra'ayin shiga ko bari ba zai shafi irin kulawar da kake samu a wannan asibitiba.

### 12) Ana biyan kudi ne?

Wannan gwajin magani kyauta ne, ko kai ko likitanka ba wanda za a biya domin shiga wannan bincike.

### 13) Wane qarin bayani za a yi min?

"London School of Hygien and Tropical Medicine" ce ta dauki nauyin wannan bincike ba masu aikin hada magani ba. Idan har muka samu qarin bayani da kan iya sauya maka/ki ra'ayi a wannan bincike za mu sanar da kai/ke. Idan kuma aka samu matsala hark a cutu a sakamakon wannan gwaji to "London School of Hygien and Tropical Medicine" za ta dauki nauyin duk wata cutuwa da ta far aba a dalilin sakaci ba. Domin kare muradunka, Kwamitin Kula da Qa'idojin Bincike [National Health Research Ethics Committee] ya bibiyi bayanan wannan gwaji a tsanaki. Kuma ya amince mu gudanar da wannan bincike.

Wannan Nazari ya sami amincewar Hukumomin kasar Najeriya:

The Director, Drug Evaluation & Research Directorate
National Agency for Food and Drug Administration and Control (NAFDAC)
Address: Oshodi Apapa Expressway, Oshodi, Lagos
Tel: + 234-435555333

The NHREC assigned number is: NHREC/01/01/2007
Approval dates: 21/05/2020to 20/05/2021.

Sakamako na qarshe zai bayyana a shafinmu na yanar gizo idan ya fito.

# TAKARDAR AMINCEWAR MAI SHA'AWAR SHIGA

**Taken bincike:** Matsayin Asprin da losartan da simbastatin a jiki majinyacin Kwarona bairos da ke a asibiti: gwajin sakamako na canki-canka a mabambantan qasashe (CRASH 19)

| | |
|---|---|
| **Sunan asibiti:** (yi amfani da manyan baqaqe) | |
| **Sunan mai sha'awar shiga** (yi amfani da manyan baqaqe) | |
| **Lambar tsabin canki-canka** (shigar da lambar zavinka/ki) | |

**1. An bani bayani game da game da wannan bincike:** na karanta (an karanta min) kuma na fahimci bayanin cikin takradar mai sha'awar shiga ta (Lambar nau'in v1.0 kawan wata 23 /04/ 2020) kuma ina da damar yin tambaya a kan bayanan. An amsa wannan daidai.

**2. Shiga bincike ne na sa-kai:** na fahimci cewa shiga wannan binciken sa –kai ne kawai ina iya fita duk a kowane lokaci ba tare da wani dalili ba kuma ba tare da duk wata kulawa ta lafiya ko 'yanci ya tavu ba.

**3. Damar bincike a kaina:** na bayar da izni duba bayanai na magani da ya dace yayin gudanar da wannan bincike, cikin sirri, ga wanda wannan asibiti ya amincewa ko "London School of Hygien and Tropical Medicine" ko kuma hukumomin da ke saka idon don ganin biciken ya tafi daidai.

**4. Damar duba bayanin lafiyata:** na amince duk wani bayanin maganina da likitocin wannan asibiti suka tattara don kula da ni a tura shi zuwa ga "London School of Hygien and Tropical Medicine". Kuma na amince duk wani bayani da ba zai bari a gane waye ni ba a tura ga masu gudanar da wannan bincike ta hanyar bayanan alumma na yanar-gizo.

**5. Bayanan da aka ajiye a kwamfiyuta:** na fahimci cewa bayanan cigaba da nake samu a wannan bincike da a adan shi a matattarar bayanai kuma za a ajiye bayanin a kan kwamfiyuta da "London School of Hygien and Tropical Medicine" ke kula da ita. Sannan na fahimci cewa wannan bayanai za a adana su cikin sirri da aminci.

**6. Damar duba takardar amincewa:** na bayar da damar yin kwafin wannan takarda bisa kwafiyuta a tura "London School of Hygien and Tropical Medicine" idan buqata ta taso.

**7. Yarda da shiga wannan aiki: na yarda na shiga cikin wannan bincike.**

| | | |
|---|---|---|
| ………………………………………… | …………………………………… | ……./……./……….. |
| Suna Mai Sha'awar Shiga Bincike (Babban Baqi) | Sa Hannu/dangwale ko alama | kwanan wata |
| ………………………………………… | …………………………………… | ……./……./……….. |
| Sunan Mai Karvar Amincewa (Babban Baqi) | Sa Hannu | kwanan wata |

**Idan mai sha'awar shiga bai iya karanta rubutu /ko sa hannu da kansu ba amma za su iya bayyana amincewa:** Na saurari karatun dalla-dalla na takardar amincewa da aka yi wa wannan mai sha'awar shiga bincike da ke da damar yin tambaya a lokacin kuma a ba shi amsa, na tabbatar ya bayyana amincewarsa cikin ganin dama.

| | | |
|---|---|---|
| ………………………………………… | …………………………………… | ……./……./……….. |
| Sunan Shaida (Babban Baqi) | Sa Hannu | kwanan wata |

The NHREC assigned number is: NHREC/01/01/2007
Approval dates: 21/05/2020to 20/05/2021.

*Kwafi daya 1 na mai sha'awar shiga daya 1 a takardar magani, na farkon kuma na fayil mai sa ido. Idan an ji tsoron tava takarda don gudun kamuwa da cutar kwarona sai a yi amfani na cikin kwafiyuta a tura wa LSHTM amma a bai wa mai sha'awar shiga kwafi guda.*

# TAKARDAR AMINCEWAR WAKILI

**Taken bincike:** Matsayin Asprin da losartan da simbastatin a jiki majinyacin Kwarona bairos da ke a asibiti: gwajin sakamako na canki-canka a mabambantan qasashe (CRASH 19)

| | |
|---|---|
| **Sunan asibiti:** (yi amfani da manyan baqaqe) | |
| **Sunan mai sha'awar shiga** (yi amfani da manyan baqaqe) | |
| **Lambar tsabin canki-canka** (shigar da lambar zavinka/ki) | |

**Idan mai sha'awar shiga ya kasa bayyana amincewa a wani lokaci saboda tsanantar jiki( misali. Rashin gudanar jinni ko rudewa ko buqatar injin jan-numfashi.):**

- Na karanta wannan bayani(ko an karanta min) kuma ina da damar tambaya
- Na fahimci cewa za a nemi mai sha'awar shiga ya tabbatar da ra'ayinsa da zarar ya samu damar yin bayani da cewa idan yana so za iya janyewa daga wannan bincike kai-tsaye ba tare da hakan ya shafi sha'anin lafiyarsa ba.
- Na yi imanin cewa idan mai sha'awar shiga ya samu dama zai amince da kansa ya shiga wannan bincike.

……………………………………………… ……………………………………….. ……../……../…………

Sunan wakili (Babban Baqi) Sa Hannu/Dangwale ko alama kwanan wata

………………………………………………

Alaqar wakili da mai sha'awar shiga

……………………………………………… ……………………………………….. ……../……../…………

Sunan Mai Karvar Amincewa (Babban Baqi) Sa Hannu Kwanan wata date

** Kwafi daya 1 na mai sha'awar shiga daya 1 a takardar magani, na farkon kuma na fayil mai sa ido. Idan an ji tsoron tava takarda don gudun kamuwa da cutar kwarona sai a yi amfani na cikin kwafiyuta a tura wa LSHTM amma a bai wa mai sha'awar shiga kwafi guda.*

The NHREC assigned number is: NHREC/01/01/2007
Approval dates: 21/05/2020to 20/05/2021.